


Wannan shi ne
Buba.




Buba yana son
karatun littattafai.



Wannan saniyar sunanta Pendo.



Pendo tana son cin karas.



Buba yana kai
Pendo kiwo idan ya
dawo daga
makaranta.




Ya kan shayar da Pendo ruwa a cikin tsabtattaccen kwano.



Baba kan zuba wa Pendo hatsi a daro ta ci.



Kuma yana tatsar madarar Pendo kullum.



Pendo na samar da madara mai tarin yawa.




Baba kan kai
madarar Pendo
shago ya sayar.



Buba na jin daɗin shan madara sabuwar tatsa kullum.



Cikin murmushi, ya
kan dafa ta ya ce,
"Na gode, Pendo!"